# 3 Yohanna

1 Dattijon nan,

Zuwa ga ƙaunataccen abokina Gayus, wanda nake ƙauna ƙwarai da gaske.

2 Abokina ƙaunatacce, ina addu'a ka sami zaman lafiya
don kome yă yi maka daidai, kamar yadda ruhunka yake
zaune lafiya. 3 Na yi farin ciki ƙwarai sa'ad da waɗansu
'yan'uwa suka zo suka yi zance game da yadda kake da
aminci ga gaskiyan nan da kuma yadda kake cin gaba cikin
gaskiyan nan. 4 Ba abin da ya fi sa ni farin ciki fiye da in ji
cewa 'ya'yana suna cikin gaskiyan nan.
5 Abokina ƙaunatacce, kana da aminci cikin abin da
kake yi wa 'yan'uwa, ko da yake su baƙi ne a gare ka.
6 Sun faɗa wa ikkilisiya game da ƙaunarka. Za ka kyauta
in ka sallame su a hanyar da ta cancanci Allah. 7 Saboda
Sunan nan ne suka fito, ba sa karɓan wani taimako daga
waɗanda ba masu bi ba. 8 Saboda haka ya kamata mu
nuna halin karɓan baƙi ga irin mutanen nan domin mu
yi aiki tare saboda gaskiyan nan.
9 Na rubuta wa ikkilisiya, amma Diyotirefes, wanda yake
son zama na farko, ya ƙi yă yi hulɗa da mu. 10 Saboda haka
in na zo, zan tone abin da yake yi, yana surutu game da
mu, yana ɓaɓɓata mu. Wannan ma bai ishe shi ba, har
yana ƙin marabtar 'yan'uwa. Yana hana waɗanda suke so
yin haka, yana ma korinsu daga ikkilisiya.
11 Abokina ƙaunatacce, kada ka yi koyi da abin da yake
mugu sai dai abin da yake nagari. Duk mai yin abin da yake

nagari daga Allah yake. Duk mai yin abin da yake mugu
bai taɓa sanin Allah ba. 12 Demetiriyus yana da shaida mai
kyau daga wurin kowa, har gaskiya kanta ma ta shaide shi.
Mu ma muna ba da shaida mai kyau a kansa, ka kuma san
cewa shaidarmu gaskiya ce.

13 Ina da abubuwa da dama da zan rubuta maka, sai dai
ba na so in yi amfani da alƙalami da inki in rubuta su. 14 Ina
fata in gan ka nan ba da daɗewa ba, za mu kuwa yi magana
fuska da fuska.

15 Salama gare ka.

Abokai a nan suna gaishe ka. Ka gai da abokai a can da
sunansu.

# Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™

# Hausa: Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™ (Bible) of Nigeria

copyright © 2020 Biblica, Inc.

Language: Hausa

Contributor: Biblica, Inc.

Biblica® Open Yoruba Contemporary Bible™
Copyright © 2009, 2017 by Biblica, Inc.
Used with permission. All rights reserved worldwide.
"Biblica" is a trademark registered in the United States Patent and Trademark Office by Biblica, Inc. Used with permission.
All content on open.bible is made available under a Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 License (http://creativecommons.org/licenses/by-sa/4.0/).
You are free to:

Share — copy and redistribute the material in any medium or format

Adapt — remix, transform, and build upon the material for any purpose, even commercially

Under the following conditions:

Attribution — You must attribute the work as follows: "Original work available for free at www.biblica.com and open.bible" Attribution statements in derivative works should not in any way suggest that we endorse you or your use of this work.

ShareAlike — If you remix, transform, or build upon the material, you must distribute your contributions under the same license as the original.

Use of trademarks: Biblica® is a trademark registered in the United States Patent and Trademark Office by Biblica, Inc. and may not be included on any derivative works. Unaltered content from open.bible must include the Biblica® trademark when distributed to others. If you alter the content in any way, you must remove the Biblica® trademark before distributing your work.
This translation is made available to you under the terms of the Creative Commons Attribution Share-Alike license 4.0.
You have permission to share and redistribute this Bible translation in any format and to make reasonable revisions and adaptations of this translation, provided that:

You include the above copyright and source information.

If you make any changes to the text, you must indicate that you did so in a way that makes it clear that the original licensor is not necessarily endorsing your changes.

If you redistribute this text, you must distribute your contributions under the same license as the original.

Pictures included with Scriptures and other documents on this site are licensed just for use with those Scriptures and documents. For other uses, please contact the respective copyright owners.

Note that in addition to the rules above, revising and adapting God's Word involves a great responsibility to be true to God's Word. See Revelation 22:18-19.

2021-11-15

---

PDF generated using Haiola and XeLaTeX on 29 Jan 2022 from source files dated 30 Dec 2021

18113be6-b3a0-530a-b78f-a25225282250